# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Cin zarafi ta hanyar lalata tsakanin al'umma a Afirka
## Kashi na takwas: Kura-kurai

Wanda ya rubuta: Chrispin Mwakideu
Wanda ya fassara: Yusuf Idris
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Fati: | 'yar shekara 16 |
| Tanko: | ɗan shekara 45 |
| Judie: | 'yar shekara 40 |
| Adams: | ɗan shekara 10 |
| MalamaTalatu: | 'yar shekara 45 |
| Wasu yara | |
| Yaro: | ɗan shekara 10 |
| Precious: | 'yar shekara 30 |
| Jammo: | ɗan shekara 45 |
| Hadiza: | 'yar shekara 30 |

**Mai gabatarwa:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin wannan shiri na "Ji Ka Karu", kashi na takwas. A cikin shirin da ya gabata Dauda ya kasa daurewa a kan yadda jama'a suke mai da su saniyar ware shi da matarshi bayan abin da ya same ta. Saboda haka sai ya yanke shawarar shi ma ya tafi ya ƙyale ta. Saura kaɗan yarinyar nan 'yar shekaru goma sha shida, wato Fati, ta faɗa wa Julie irin abubuwan da suke faruwa da ita. Amma sai Malam Tanko wanda da ma shi ne yake cin zarafinta ya tsai da ta daga tona mai asiri. A wani ɓangare kuma jami'an 'yan sanda sun damƙe Kawu Jammo, bayan yaron nan Adams ya faɗa wa malamarsu cewa, Kawu Jammon yana cin zarafinshi ta hanyar yin lalata da shi. Me zai faru nan gaba? Za mu ji a cikin shirin na yau mai taken "Ku miƙe". Za mu faro ne daga ofishin Malam Tanko wanda ya harzuƙa saboda Fati ta yi ƙoƙarin faɗa wa Julie abubuwa da ke faruwa da ita.

**Fitowa ta 1: A ofishin Malam Tanko a makaranta**

**Tanko:** Fati! Me kika faɗa wa wannan muguwar matar? Eee?! … Na ce ki faɗa min! Idan kuma ba ki faɗa min ba, zan kore ki daga makarantar nan. Kin san cewa ina da ƙarfin da zan iya yin haka ko? Sannan me mahaifiyarki za ta ce? … Ina magana da ke ne! Yarinyar banza kawai! Ba ki jin daɗi ko yaushe ina sa kina fin kowa a aji? Na ba ki maki ɗari bisa ɗari a *biology* duk da cewa sha biyar kawai kika samu! Sannan da haka za ki saka min? Ta hanyar cin amanata ke nan? Ta faɗa wa wasu sirrinmu?

**Fati:** Amma… amma… Malam Tanko…

**Tanko:** Zauna, zauna! Fati, na ce ki zauna!

**Fati:** Don Allah… don Allah kar ka yi… Malam Tanko, ba na jin daɗi idan kana taɓa ni… idan kana… A'a!... Don Allah ka

daina!

**Julie:** Ka buɗe ƙofar nan Malam Tanko, na ji duk abin da kake faɗa wa Fati. Ka buɗe ƙofar nan kafin in kira maka 'yan sanda! … Fati! Ba abin da ya same ki ko?

**Fati:** E… ina ganin haka…

**Julie:** Ya yi kyau. Tanko, ta ƙare maka daga yau. Ka buɗe ƙofar nan. Kuma lokaci ya yi da za ka fuskanci hukunci a kan abin da ka yi.

**Tanko:** Madam Julie, ina ganin akwai ɗan kuskure a nan. Ban san abin da kike tunani ba, amma ni ai…

**Julie:** Kar ma ka yi tunanin cewa za ka ƙaryata cewa ba abin da ya faru, Malam Tanko! Kalli halin da take ciki! Fati kar ki damu, ba abin da zai same ki. Mai da rigarki ki jira ni a waje.

**Tanko:** Shi ke nan, shi ke nan, na yarda na aikata. Amma ai ba da niyyar na cutar da ita ba ne. Don Allah ki yafe min. Kar ki kira 'yan sanda! Don Allah ki tausaya min. Ina da mata da yara. Ki taimake ni kar su gane wannan abin, ina roƙonki don Allah!

**Julie:** Da ka yi tunanin haka kafin ka ci zarafin ɗalibarka. Allah kaɗai ya san ko ɗalibai nawa ne ka ci zarafinsu kuma suka kasa yin magana.

**Tanko:** A'a, na rantse Fati ce kaɗai! Ban taɓa yin haka da wata ɗaliba ba tun da nake.

**Julie:** Ban yi tsammanin haka ba. Saura kaɗan ma ka mai da ni sakarya, Tanko. Amma ka san wani abu? Asirinka ya tonu! Kuma sai na tabbatar da ka fuskanci hukunci mai tsanani a kan abin da ka yi wa Fati.

**Tanko:** Shi ke nan, na yarda da abin da na aikata. Na san cewa abin da nake yi bai kamata ba, amma na kasa dainawa. Ina buƙatar taimako kuma na san za ki iya taimakona, Madam Julie. Don Allah ki yi min haƙuri!

**Julie:** Haƙuri? Don ka ci gaba da cin zarafin wasu? Ka manta kawai! Kai malaminta ne. An ba ka amanar waɗannan yaran ne domin ka koyar da su, ba don ka ci zarafinsu ba. Dole ne ma 'yan sanda su shigo cikin wannan maganar.

**Tanko:** 'Yan sanda? Don Allah ki yi haƙuri, Malama Julie!

**Julie:** Ka makara. Da zaran mun fita daga nan ni da Fati, zan wuce ofishin 'yan sanda ne domin in kai rahoton abin da ka yi, daga nan kuma sai hukuma ta yi aikinta.

**Mai ba da labari:**

Julie ta cika alƙawarinta. Nan take aka tilasta wa Malam Tanko ya ajiye aikinshi na koyarwa. Kuma zai fuskanci zargin da ake yi mai na aikata laifi a kotu. Amma kuna ganin cewa abin da Julie ta yi ya yi daidai? Ko kuwa kuna ganin ya kamata masu aikata irin wannan laifin in sun roƙi a yafe musu a yafe musun?

A yayin da kuke tunanin amsar da za ku bayar, bari mu koma wurin yaron nan Adams. Ya koma makaranta kuma yana ƙoƙarin ci gaba da rayuwarshi, amma kamar sauran waɗanda irin wannan abin ya faru da su, ci gaba da yin rayuwarshi kamar da na neman ya zama da wahala.

**Fitowa ta 2: A makarantar su Adams**

**Wasu yara:** Adams sakarai ne… Adams sakarai ne…

**Adams:** Ku ƙyale ni! Zan kai ƙaranku wurin Malama Talatu.

**Wasu yara:** Adams sakarai ne… Adams sakarai ne…

**Malama Talatu:** Kai! Kai! Ku daina mana! Me kuke yi haka? Ku zo nan, ku zo nan dukanku! Adams, kai ma ka zo! Me suke cewa dai kai?

**Adams:** Wai suna ce da ni sakarai.

**Malama Talatu:** Haka ne? To me ya sa kuke kiran Adams sakarai ne? Ku ba ni amsa mana! Me ya sa za ku riƙa kiransa da suna sakarai?

**Yaro:** Saboda ba ya zama tare da mu, sai dai ya zauna can shi kaɗai. Amma wasa muke yi mishi, ki yi haƙuri, Malama Talatu.

**Malama Talatu:** To ku saurare ni ku ji! Ba ma irin wannan wasa a nan. Ba abin wasa ba ne wannan. Saboda haka ina so ku ba shi haƙuri, kuma idan na sake jin kun kira shi ko kun kira wani yaro sakarai, ba zan yi muku da wasa ba. Kun ji ko?

**Yara:** Mun ji, Malama Talatu!

**Malama Talatu:** To, ku ba shi haƙuri!

**Yara:** Ka yi haƙuri, Adams. Ka yi haƙuri!

**Yaro:** Adams, ba za ka zo ka yi wasa da mu ba?

**Adams:** Shi ke nan.

**Mai ba da labari:**
Malama Talatu na iyakar bakin ƙoƙarinta a kan Adams, amma ta san cewa al'amarin zai ɗan yi wuya. Bayan 'yan kwanaki sai aka kai Kawu Jammo kotu, kuma da shaidar da Malama Talatu ta bayar, da shi kanshi Adams, sai kotu ta same shi da laifi kuma ta yanke mai hukuncin zaman gidan yari na shekaru biyar. Kwana ɗaya bayan an yanke masa hukunci, sai mahaifiyar Adams wato Precious ta kai wa tsohon saurayin nata ziyara.

**Fitowa ta 3: A gidan yari**

**Jammo:** A'a masoyiyar! Ashe dai kin yi *missing* ɗina.

**Precious:** Maganar banza! Matsiyaci, mugu, shaiɗani kawai!

**Jammo:** Haba Precious, kar dai ki ce min kin yarda da abubuwan da ɗanki ya faɗa a kotu? Ni ne fa! Jammonki! Na yi…

**Precious:** Rufe min baki! Ba na so in ƙara ganinka a rayuwata. Ba zan ƙara yarda da kai ba! Ina ta kare ka a gaban malamar su Adams, ashe kana ta lalata min yaro ban sani ba. Haba! Yaya aka yi na zama sakarya haka!

**Jammo:** Ba laifinki ba ne Precious, ba wanda zai ƙi amincewa da ni. Amma kar ki damu, shekara biyar ne kawai, idan kuma na nuna nadama ina iya fitowa bayan shekara biyu. Nan ba da daɗewa ba zan gan ki.

**Precious:** Ka haukace! Kai mahaukaci ne! Kana da taɓuwa a kanka! Ba na so in ƙara ganinka! Ina roƙon Allah ya sa ka ruɓe a gidan yari!

**Jammo:** Haba Precious, ba dai da gaske kike yi ba ko? Ban kai yadda kike tunanin na lalace ba. Ba za ki iya zama ba tare da ni ba, ke ma kin san ba za ki iya ba!

**Mai ba da labari:**

Wanshekare sai jaridu suka fito da labarin kame Jammo. Mutane da yawa sun yi mamakin yadda wai a ce mutumin da ya aikata irin wannan mummunan laifi, da ya shafi rayuwar yaro ɗan karami, an ɗaure shi na tsawon shekaru biyar kacal. Ita ma Julie ta karanta labarin a kan hanyarta ta zuwa ofishinta.

**Fitowa ta 4: A cibiyar Julie**

**Julie:** Wai kun ji irin wannan abu? Wannan ai ba ƙaramin wulaƙanci ba ne! Ku yi haƙuri na yi raina ne ya ɓaci, amma abin ne ya ba ni mamaki. Ku saurara ku ji abin da zan karanto daga jaridar nan: "Wani mutum da ya ci zarafin yaro ƙarami ya sami ɗaurin shekaru biyar a gidan yari." … Ku bari in gama karantowa tukuna. "Babban alƙalin ƙasar nan ya ɗaure wani mutum da aka kama shi da laifin yin luwaɗi da wani yaro ɗan shekaru goma na tsawon shekaru biyar. Mutumin wanda saurayin mahaifiyar yaron ne ya yi ta cin zarafin yaron ne a lokacin da mahaifiyar ke wurin aiki. Wanda ake zargin dai bai nuna damuwa ba ko da-na-sani bisa laifin da ya aikata a lokacin da ake karanta mai hukuncin da aka yanke masa. Irin waɗannan laifuffuka dai na cin zarafi da fyaɗe sai ƙaruwa suke yi a wannan ƙasar

tamu." …

Ba zan yarda da wannan ba. Dokokin ƙasarmu a kan cin zarafin mata ba su da ƙarfi sosai. Dole sai an yi wani abu a kan wannan. Ya kamata gwamnati ta ƙara ƙarfafa dokokin, kuma su san cewa suna bayan waɗanda abin ke shafa! Zan kira wani babban taron 'yan jaridu, kuma ina gayyatar kowannenku. Wasu daga cikinku na iya shiryawa don su faɗi labarin irin abin da ya faru da su, wasu kuma na iya zuwa taron kawai ba sai sun faɗi labarinsu ba. Ya kamata mu miƙe don mu yaƙi cin zarafin mata! Ina ganin wasu daga cikinku sun kusa shiryawa don su ba da labarinsu.

**Hadiza:** Na shirya! Sunana Hadiza. Na shirya in ba da labarina.

**Mai gabatarwa:**

Da haka kuma muka kammala shirin na yau. Me zai faru da Fati, da yake a yanzu Malam Tanko ya ajiye aikinshi a makarantar? Shin Julie za ta yi nasarar ganin cewa ta sa an ƙara tsaurara dokar cin zarafi da fyaɗe? Ku kasance da mu a shiri na gaba. Idan kuna muradin sake sauraron wannan shirin kuna iya tuntuɓar adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Ko kuma a tattauna da mu ta shafinmu na Facebook. Sai mun sadu a shiri na gaba. Ku huta lafiya.